Hausa هوسا

# YARO MUSULMI

*LITTAFI NE DA YA KUNSHI BAYANIN MUSULUNCI DA HALAYYARSA, GA YARA MUSULMAI*


Tanadar
Gungun Doktocin ilimi na kasar Aljeriya

Fitarwar
Sayit INA YIN WASA INA KOYON ILIMI



alsarhaan.com

mahadsunnah.com

بسم الله الرحمن الرحيم

# KASO NA FARKO 1


## DOMIN BUNKASA IMANI

Ni Musulmi ne.

**ALLAH SHINE UBANGIJINA.**
**KUMA MUHAMMADU -TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU KARA TABBATA A GARE SHI- SHINE ANNABINA NE.**
**KUMA MUSULUNCI SHINE ADDININA.**

Ni ina son Allah Ta'alah;
Saboda shine Ubangijin Talikai, Mai rahama Mai jinkai, Mamallakin ranar sakamako.
Kuma saboda shi ne ya halitta ni, ya azurta ni, Kuma saboda shine ya sanya ni Musulmi.

### Allah ya fada a cikin Alkur'ani:



**Da sunan Allah Mai rahama Mai jinkai. 1**
**.Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikai 2**
**.Mai rahama Mai jinkai 3**
**.Mamallakin ranar sakamako 4**
**.A kai muke bautawa, Kuma daga gare ka muke neman taimako 5**
**.Ka shiryar da mu hanya madaidaiciya 6**
**Hanyar wadanda ka yi wa ni'ima; ba wadanda aka yi fushi akansu ba, Kuma ba !batattu ba 7**

(Suratul Fatiha)

**Kuma ina son Annabi ne -sallal Lahu alaiho wa sallama-**
**Saboda Allah ya turo shi gare mu; sai ya sanar da mu Allah, kuma ya ilmantar da mu Alkur'ani.**

Kuma saboda shi Annabi -sallal Lahu alaihi wa sallama- Mai tausayi ne Mai jinkai, Dabi'unsa masu girma ne, sifofinsa masu kyau ne,

**Allah Ta'alah yake fada akansa:**

(Kuma lallai kai kana kan dabi'u masu girma)

Suratul Kalam

Kuma ya ce:

**(Dangane da Muminai Mai tausayi ne Mai jinkai)**

Suratut Tauba.

Kuma Allah Ta'alah ya ce:

Kuma lallai mun baka Alkausar 1 Tafki ko alheri mai tarin yawa 2 Sai ka yi sallah ga Ubangijinka, Kuma ka yi suka, Kuma Mai aibantaka shine Mai yankakken baya 3

Suratul Kausar

## Kuma ina son addinin Musulunci

**Saboda shine addinin gaskiya, wanda Allah ya yarje mana shi, Kuma Annabinmu Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya zo mana da shi.**
**Kuma saboda shine addinin da idan aka yi riko da shi Mutum zai shiga Aljannah, idan kuma Mutum ya yi watsi da shi zai shiga Wuta.**

Allah Ta'alah ya ce:

Ina rantsuwa da zamani 1 Lallai Mutum yana cikin hasara, 2 Saidai wadanda suka yi imani, kuma suka aikata aiki na kwarai, Kuma suka yi wasici da gaskiya, Kuma suka yi wasici da hakuri 3

Suratul Asr

## RUKUNNAN IMANI GUDA 6 NE

6

1. Imani da Allah.
2. Imani da Mala'iku.
3. Imani da littatafai.
4. Imani da Manzanni.
5. Imani da ranar karshe.
6. Imani da kaddara mai kyanta da mummunanta.

## Kuma RUKUNNAN MUSULUNCI BIYAR NE:

5

1. Shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma annabi Muhammadu manzon Allah ne
2. Tsayar da sallah.
3. Bada zakka.
4. Azumin watan Ramadhana.
5. Da ziyartar dakin Allah mai alfarma (hajji).

KUMA INA SON DUKKAN ABINDA ALLAH YAKE SONSA, DA MANZONSA SAW.

KUMA INA KIN DUKKAN ABINDA ALLAH DA MANZONSA SUKE KINSA.



# KASO NA BIYU

# 2

# SALLATA




*Allah ya halitta mu domin yin bauta a gare shi, Shi kadai ba tare da abokin tarayya ba, don haka, ba za mu yi bauta ga waninsa ba, ba za mu roki wanin Allah Ta'alah ba.*

Kuma mafi girman ibada ita ce:

SALLAH

# 5 Kuma salloli guda biyar ne



| | | |
|---|---|---|
| Zan sallace ta raka'oi biyu. | ASUBA | 2 |
| Zan yi raka'oi hudu. | AZAHAR | 4 |
| Zan yi raka'oi hudu. | LA'ASAR | 4 |
| Zan yi raka'oi uku. | MAGRIBA | 3 |
| Zan yi raka'oi hudu. | ISHA'I | 4 |



Kuma zan kiyaye salloli akan lokattansu,
Kuma zan rika yinsu da khushu'i.



Kuma zan yi alwala gabanin yin sallah, kuma har abada ba zan yi sallah ba tare da alwala ba.



# KASO NA UKU: 3

# DABIY'ATA

**Allah yana son kyawawan halaye, Kuma yana kin munanan halaye. Kuma Annabi -Sallal Lahu alaihi wa sallama- ya zo ne domin ya cike (wa halittu) dabi'u kyawawa**

**Don haka, Ya wajaba akaina na sifantu da dabi'u masu kyau,**
kamar gaskiya, da cika alkawari, da amana, da gwarzanta, da kyauta, da kyakkyawan zance, da girmama Malami, da Mai yawan shekaru (babba).

**Kuma na nisanci mummunan halaye,**
da ha'inci, da nuna rauni, da rowa, da yasassun magana, da rashin girmama ..Mutane

*Saboda Annabi -Sallal Lahu alaihi wa sallama- yana cewa:*

Lallai wanda ya fi kusancin wajen zama da ni a cikinku, ranar Kiyama, shine: Wanda ya fi ku kyawawan dabi'u a Duniya

# RUFEWA

Ilimi haske ne, Shi kuwa Jahilci duhu ne.

Don haka, zan dage wajen NEMAN ILIMI, Kuma zan yi kokari wajen samo shi, don Ubangijina ya yarda da ni, Kuma ya shigar da ni Aljannah.

Kuma yin zikiri shine garkuwa ga Musulmi

Don haka; zan kiyaye lamarin zikirin safiya da maraice, Kuma daga cikinsu akwai:- AYATUL KURSIYYU, da SURATUL IKHLAAS, da surarorin neman tsari guda biyu (wato FALAK da NAAS).

Shi kuma ADDU'A shine mabudin cin nasara da samun babban rabo.

Don haka; Zan yawaita rokon Allah a cikin dukkan lokatai, da cikin sujjada, da bayan kiran sallah, da kuma a tsakar dare.

Kuma yana daga cikin MUHIMMAN ADDU'OI:

Ya Allah! Ka shiryad da ni, kuma ka datar da ni!

Ya Allah! Ka kara mini ilimi!

Ya Allah! Ka gafarta mini da iyayena biyu, Kuma ka musu rahama!

Ya Allah! Ka bani mai kyau a Duniya, A lahira shima mai kyau, Kuma ka tsare ni daga azabar Wuta.

**Littafin ya cika,**

**da godiyar Allah!**

Littafin "YARO MUSULMI (الطفل المسلم) ": littafi ne da yazo cikin harshen larabci, wanda shafin yanar gizo-gizo mai suna: mauki'u Al'abu wa ata'allamu (wato, ina koya daga wasan da nake yi) wanda shehun Malami Dr. Haisam Sarhan yake aikin bada kulawa a gare shi, kuma littafin ya kunshi manufofin musulunci da halayyarsa ga Yaro Musulmi, littafin yana da ban kaye, kuma an yi bugunsa cikin yanayi mai kyau wanda yake sanya Mutum dadin rai, yake kwadaitar da .makaranci yawaita karanta shi